# NAJERIYA | NIGERIA

## USCIRF– RECOMMENDED FOR COUNTRIES OF PARTICULAR CONCERN (CPC)

Hukumar Ƴancin Addini ta Ƙasa da Ƙasa ta U.S. (USCIRF) wata hukuma ce mai zaman kanta, ta gwamnatin tarayyar Amurka da ke sanya ido kan dama ta ƴancin addini ko aƙida a ƙasashen waje. USCIRF, wadda Dokar Ƴancin Addini ta Kasa da Ƙasa (IRFA) ta 1998 ta ƙirƙira, tana amfani da tsarukan ƙasa da ƙasa domin sanya ido kan keta ƴancin addini ko aƙida a ƙasashen waje sannna ta bayar da shawarwari kan manufofin gwamnati ga shugaban ƙasa, ministan harkokin ƙasashen waje, da Majalisar Dokoki. USCIRF ma'aikata ce mai zaman kanta da ta keɓanta kuma ta bambanta da Ma'aikatar Harkokin Ƙasashen waje ta Amurka. Rahoton Shekara-shekara na 2021 yana matsayin fara aikin shekar ne da Kwamishinoni da ƙwararrun ma'aikata ke yi domin tattara cin zarafi da aka yi tare da bayar da shawarwari kan manufofin gwamnati mai zaman kansa ga gwamnatin Amurka. Rahoton Shekara-shekara na 2021 ya haɗe tsawon lokaci daga Junairu 2020 zuwa Disamba 2020, ko da yake a wasu halayen ana ambatar waɗansu muhimman abubuwa da suka faru kafin ko bayan wannan lokacin. Domin ƙarin bayani game da USCIRF, duba shafin yanar-gizo a nan, ko a tuntuɓi USCIRF kai tsaye a 202-523-3240.

### MUHIMMAN SAKAMAKO

A 2020, yanayin ƴancin addini a Najeriya ya taɓarɓare, inda gwamnati da waɗanda ba gwamnati ba suka aikata mugayen laifukan keta haƙin ƴancin addini ko aƙida. Duk da cewa kundin tsarin mulkin Najeriya ya na kare ƴancin addini da aƙida, ƴan kasar Najeriya sun fuskanci rikici daga tsagerun Islama da waɗansu masu ɗauke da makamai da ba na gwamnati ba, gami da wariya, tsarewa ba bisa ƙa'ida ba, tare da yanke hukumce-hukuncen kisa kan laifukan zagin addini daga hukumomi.

Kotunan Shari'a da gwamnati ta kafa sun yanke tsauraran hukunce-hukunce a kan mutane da dama da aka kama da laifin zagin addini, da ya haɗa da da yanke hukuncin kisa a kan mawaƙi ɗan shekaru 22 Yahaya Sharif-Aminu, koda yake wata babbar kotu ta buƙaci a sake duba shri'ar Sharif-Aminu. Hukumomin gwamnati sun kama fitaccen mai fafutukar kare ƴanci Mubarak Bala, da aka ce yana da alaƙa da bayyanar da aƙidar sa ta ƴancin ɗan-adam a shafin sada zumunta. Bala ya cigaba da kasancewa a tsare ba tare da gurfanar da shi gaban kotu ba, kuma hukumomi sun taƙaice masa ganawa da lauyoyinsa.

Ƙungiyoyin Tsagerun Islama a Najeriya sun cigaba da keta ƴancin addini a arewa-maso-gabas kuma sun yaɗu zuwa ɓangarorin yankin arewa-maso-yamma na ƙasar. Wasu ƴan Boko Haram da na ƙungiyar ISWAP da ke yankin Afirka ta Yamma sun kama tare da kashe mutane da dama saboda bambancin addininsu. Mayaƙan Boko Haram sun kashe wani ƙaramin shugaban Kungiyar Kiristoci ta Najeriya (CAN) a Jihar Adamawa saboda ya ƙi ya canja addininsa, yayin da mayaƙan ISWAP su ka kashe ma'aikatan jin ƙai biyar a matsayin gargaɗi ga "duk waɗanda a ke amfani da su domin mayar da Musulmai zuwa Kiristoci." Haka kuma Mayaƙan Jihadi sun gudanar da hare-hare da dama a kan bukukuwan addini: a watan Mayu sun kai hari kan ƙauyawa da ke shirin buɗe-baki na azimin Ramadan, suka kashe mutane 20, kuma a watan Yuli sun kai hari kan mutanen gari da ke taruwa don yin Sallar Idin Layya a Maiduguri.

A tsakiyar ƙasar, waɗansu ƙungiyoyin ƴan bindiga da ba na gwamnati ba sun gudanar da hare-hare a kan wuraren ibada, bukukuwan addini, da shuwagabannin addini. An taɓa al'ummar Kiristoci musamman a nan Yankin Tsakiyar ƙasar, inda ƴan bindiga da ba na gwamnati ba su ka kai hari kan aƙalla coci 11 da bukukuwan kirista. Waɗanda suka tsira sun bayar da labarin cewa ƙungiyoyin 'yan bindiga masu alaƙa da Fulani sun yi amfani da ikirarin addini yayin da suke kai ɗimbin hare-hare a ƙauyukan da Kiristoci suka fi yawa a Jihar Kaduna. An ruwaito cewa masu garkuwa da mutane ma suna kai wa Kiristoci hari da gangan domin yin garkuwa da kuma kashe su. Gwamnatin Najeriyan ta cigaba da gazawa wurin binciken waɗannan hare-hare tare da hukuntar da masu laifi, wanda ke nuni da wani matsayi na matsalar rashin nuna damuwa daga ɓangaren jami'an gwamnati.

### SHAWARWARI GA GWAMNATIN AMURKA

- A sake sanya Najeriya a matsayin "ƙasar da za a baiwa kulawar musamman" ko CPC, saboda aikatawa da kuma bari ana cigaba da aikata, mummunan keta ƴancin addini, kamar yadda Dokar Yancin Addini ta Kasa da Ƙasa (IRFA) ta fasalta, da kuma sake saka Boko Haram da sanya ISWAP a matsayin "kungiyoyi da za a baiwa kulawar musamman" ko EPCs, saboda aikatawa da kuma bari ana cigaba da aikata, mummunan keta ƴancin addini, kamar yadda Dokar Yancin Addini ta Kasa da Ƙasa IRFA ta fasalta;
- A ƙulla wata yarjejeniya mai aiki, kamar yadda sashe na 405(c) na IRFA ya umarta, sannan a samar da tallafin kuɗi da fasaha masu alaƙa domin tilastawa gwamnatin Najeriya ta dauki muhimman matakai domin warware matsalar keta ƴancin addini, da ya haɗa da amma bai taƙaita ba ga:

- Bunƙasa horaswa ga jami'ai, sojoji, da jami'an ƴan sanda a kan yaki da kalaman ƙiyayya bisa nau'in addini, ɗaukan matakin daƙile tarzomar ƙabilanci, bayar da rahoton tarzoma a kan mabiya addini, tare da tuhumar jami'an tsaro da ake zargi da amfani da ƙarfi ba bisa ƙa'ida ba da kuma wasu nau'ukan cin zarafin ɗan-adam;
    - Yaɗawa da kuma faɗaɗa samun adalci da kuma ƙarfafa kotunan da ba na addini ba a wuraren da barazanar bambancin ƙabilanci da addini ke da ƙarfi tare yawan aukuwar tarzoma, aikata laifuka, da hukuncin 'yan tarzoma;
    - Ƙara yawan kuɗi domin gyara ɓangaren tsaro da shirin dokoki da kuma saka masana addini a cikin shirye-shiryen tsaro da adalci;
    - Ware kuɗi domin shirye-shirye da suka haɗa ƙungiyoyin farar hula, jami'an tsaro, da hukumomi a cikin yunƙurin haɗin gwiwa domin kare wuraren ibada da waɗansu tsarkakakkun wurare;
- A gudanar da cikakkiyar bita a kan dukkan tallafin jin ƙai na Amurka ga Najeria da kuma tasirinsu ga yanayin ƴancin addini a ƙasar;
- A ƙirƙiro wasu dabarun cikin gida da kuma yin tattaunawar diflomasiyya da muhimman hukumomin ƙananan hukumomi a yankunan da a ke yawaita samun tarzomar da hukuma ta ingiza ko ta goyi baya domin daidaita ayyukan hukuma su dace da kundin tsarin mulki da yarjejeniyoyin ƙasa da ƙasa;
- Ƙarfafa ɓangaren hulɗa da jama'a na Ofishin Jikadancin U.S. a Abuja domin lura da yanayin cigaban ƴancin addini a Najeriya a bainar jama'a, tare da yin jawabi a kan shari'ar kotu da suka shafi firsinoni masu fafutukar addini, tare da ɗauka muryoyin ƴan ƙasa masu kira ga tsarin ƴancin addini.

### MUHIMMAN ABUBUWAN USCIRF & AIYUKA

- *Sabon Bayanin Kasa*: Yanayin Ƴancin Addini a Najeriya a 2020
- *Gaskiyar Lamari:* Rikice-rikicen Addini da Al'ummun Fulani a Yammaci da Tsakiyar Afirka
- *Karɓar Aikin Fursinonin 'Yancin Ra'ayi:* *Mubarak Bala* da *Yahaya Sharif-Aminu*

## Gabatarwa

Najeriya ce ƙasa mafi yawan jama'a a Afirka, mai yawan jama'a kwatankwacin miliyan 219. Daga ciki waɗanna, kwatankwacin kashi 53.5 bisa ɗari musulmi ne, kashi 45.9 bisa ɗari Kirista ne sannan kashi 0.6 bisa ɗari mabiya addinan da suka haɗa da atheism, Baha'ism, Judaism, Hinduism, Buddhism, da addinan gargajiya na Afirka.

Kundin Tsarin Mulki na 1999 na kare ƴancin addini ko aƙida kuma ya haramta wa ƙasar samar da wani addinin ƙasa da kuma nuna bambanci dangane da addini. Kundin Dokar Laifuka na Najeriya ya haɗa da hukuncin ɗauri da ya kai shekaru biyu saboda zagin addinin wani. Bugu da ƙari, jihohin arewa 12 masu yawan Musulmi na amfani da Shari'ar Musulunci na dokokin laifuka da na iyali tare da dokokin farar hula da na gargajiya; waɗannan dokokin shari'a sun haramta zagin addini.

Addini a Najeriya yana da matuƙar tasiri a rayuwar zamantakewa da siyasa. Akwai kuma matuƙar rarrabuwar kai da rashin yarda. Sau da yawa, tashin hankalin addini yana haɗewa da matsayin kabila, inda yake ta'azzara rikicin ƙabilanci da addini wanda duka al'amuran addini da ƙabilar waɗanda aka yi wa da na waɗanda suka aikata ke jawo wa.

Gwamnatin Najeriya na ƙaddamar da hare-haren soja a kan Boko Haram da ISWAP a arewa maso gabashin ƙasar. Duk da ikirarin gwamnatin tarayya cewa ta kawar da Boko Haram, waɗannan ƙungiyoyin na cigaba da zama barazana ga fararen hula da ƴancin addini a yankin Tafkin Cadi. An ruwaito ayyukan keta haƙin dan-adam da ma'aikatan yaki da ta'addaci na Najeriya ke yi ya ƙara zafafa rashin tsaro tare da jefa rayuwar fararen hula cikin haɗari.

### Hare-hare a kan Ɗakunan Bauta da bukukuwan Addini

A watan Faburairu, mayaƙan Boko Haram sun kai hari a Garkida, wani gari da a ka sani a matsayin tushen cocin Church of the Brethren a ƙasar, inda su ka ƙona aƙalla coci biyar.. A wani jerin hare-haren a Jihar Kaduna a watan Maris, wasu da a ke zargin mayaƙan Fulani ne sun ƙona coci huɗu. A watan Afrilu, wasu mutane ɗauke da makamai da a ke zargin su na da alaƙa da mayaƙan Fulani sun kai hari kan wani bikin auren Kirista a Jihar Neja, inda su ka kashe mutane 12 kuma su ka yi garkuwa da amaryar da angon. A watan Yuli, waɗansu mutane ɗauke da makamai da ba a san ko su wanene ba sun kashe mutane 18 a wata walimar ɗaurin auren Kirista a Jihar Kaduna tare da raunana wasu mutane 30.

A watan Mayu, wasu da aka ce masu tsaurarran ra'ayin musulunci ne sun kai hari a wani yanki yayin da mutane ke shirin

buɗe-baki na azimin Ramadan, inda su ka kashe akalla mutane 20. A dai watan kuma, waɗansu mayaƙan sun kai hari a birnin Maiduguri yayin da mutane ke shirin bukukuwan Idin Layya, inda su ka kashe mutane huɗu tare da raunata waɗansu mutane uku. A watan Oktoba, waɗansu masu laikata aifi da ba a san ko su wanene ba sun ƙona masallatai biyu a Enugu da ke kudancin ƙasar.

## Mayaƙa Tsatsauran Ra'ayin Islama

Ƙungiyoyin mayaƙan Islama a arewacin Najeriya na cigaba da riƙe wadansu yankuna da kuma aikata munanan hare-hare da keta haƙin ɗan-adam a arewa maso gabas ɗin Najeriya da kuma a faɗin yankin Tafkin Chadi.  Bugu da ƙari, waɗannan ƙungiyoyi sun faɗaɗa yankunansu zuwa yamma, inda yanzu ISWAP ke gudanar da aiyukanta a Jihar Sokoto kuma Boko Haram na aiki a Jihar Kaduna.

Mayaƙan ISWAP sun yi garkuwa tare da kashe Ropvil Daciya Dalep, wani ɗalibin jami'ar Kirista, a watan Janairu; suka yi garkuwa da wani limamin Kirista da mata biyu a Jihar Borno a watan Oktoba; kuma suka kashe ma'aikatan jin ƙai biyar a matsayin gargaɗi zuwa ga "duk waɗanda a ke amfani da su domin mayar d Musulmai zuwa addinin Kirista."  Mayaƙan Boko Haram sun yi garkuwa da Reverend Lawan Andimi, ƙaramin shugaban CAN a Jihar Adamawa, daga baya su ka kashe shi, saboda ya ki canja addininsa. A watan Disamba, bayan barazanar kai hari a kan Kiristoci yayin bikin Kirsimeti, mayaƙan Boko Haram sun kai hare-hare uku a kan yankunan Kiristoci a arewacin Najeriya, inda suka kashe mutane 12 da kuma garkuwa da wani mai wa'azin kirista. Haka kuma, a watan Janairu, ƙungiyar mayaƙan Ansaru sun sake bayyana a Jihar Neja a karo na farko tun 2013, tare da ɗaukan alhakin wani hari a kan "masu ridda" a watan Agusta.

## Fursunonin 'yancin ra'ayi na Addini

A 2020, hukumomi sun keta ƴancin addini ko aƙida na ƴan Najeriya da dama, da ya haɗa da ta hanyar faɗaɗa aiwatar da dokokin zagin addini idan a ka kwatanta da shekarar da ta gabata. A watan Agusta, wata kotun Shari'a a Jihar Kano ta sami Yahaya Sharif-Aminu da laifin zagin addini bisa ɓatanci ga Annabi Muhammad a wani saƙon WhatsApp tare da yanke masa hukuncin kisa- daga baya wata babbar kotu ta soke hukuncin tare da neman a sake gudanar da shari'ar. Haka kuma hukumomin Kano sun sami Omar Farouk ɗan shekaru 16 da laifin zagin addini kuma an tsare shi na tsawon shekarar, duk da yake an yi watsi da hukncin da a ka yanke masa a farkon 2021 sannan an sake shi.

Ƴan sanda suma sun kama wani fitaccen ɗan rajin rashin addini Mubarak Bala a watan Afrilu 2020 bayan wata gamayyar lauyoyi a Jihar Kano ta shigar da ƙorafi tana zargin sa da yin ɓatanci ga Annabi Muhammad a Facebook. Har tsawon sama da watanni takwas, hukumar ƴan sanda ta Kano ta tsare Bala ba tare da tuhuma ba, tare da taƙaita ma sa ganawa da lauyoyinsa da kuma ƙin samar da shaidar wurin da yake da yanayin lafiyarsa ga iyalansa.  A watan Disamba, bayan tsarewa ta dogon lokaci, wata kotun tarayya ta bayyana tsarewar da aka yi wa Bala a matsayin abin da ya saɓa wa kundin tsarin mulki tare da umartar a sake shi- sai dai kuma, har zuwa ƙarshen 2020, Bala ya kasance a tsare hannun hukumar ƴan sanda ta Kano duk da wannan umarni.

## MUHIMMAN MANUFOFIN AMURKA

A watan Disambar 2019, Ma'aikatar Harkokin Ƙasashen Waje ta Amurka ta sanya Najeriya a karo na farko a cikin Jerin Abin Dubawa saboda aikatawa ko bari ana aikata mummunan keta 'yancin addini ƙarƙashin kundin IRFA. Bayan shekara ɗaya, a ranar 2 ga Disamba, 2020, Ma'aikatar Harkokin Ƙasashen waje ta Amurka ta sanya Najeriya a matsayin CPC saboda aikatawa ko bari a aikata musamman mummunan keta 'yancin addini ƙarƙashin IRFA, matakin da USCIRF ta bada shawara a riƙa yi duk shekara tun daga 2009. Sai dai kuma, a lokacin da ta ayyana CPC, ma'aikatar harkokin ƙasashen waje taɗaga ƙafa a kan duk wani takunkumi mai alaƙa kamar yadda ya ke a cikin "muhimmiyar manufa Amurka " ƙarƙashin Sashe na 407 na IRFA.

Sakamakon binciken Amurka a Najeriya ya cigaba da bada fifiko ga tallafin jin ƙai fifiko da bunƙasa tattalin arziki.  A watan Nuwamba, Amurka da Najeriya sun karɓi wani taron gamayyar ƙin amincewa da ƙungiyar Islamic State da kuma jaddada da ƙudurinsu na murƙushe Boko Haram da ISWAP. Yunƙurin jakadancin Amurka a Najeriya ya haɗa da shirin warware rikici ta lumana a yankunan da ke fama da matuƙar rikice-rikice da sanya ido kan shari'ar fursunoni 'yancin ra'ayi na addini.

A watan Nuwamba, biyo bayan muzgunawa masu zanga-zangar lumana da ke zanga-zanga a kan cin zarafi da ƴansanda ke yi, Ƙungiyar 'Yan Majalisar Amurka Baƙaken fata ta aika wa Shugaban Ƙasa Muhammadu Buhari wata wasiƙa da ke yin yin alla-wadai da cin zarafin da hukumomi su ke yi a kan masu zanga-zangar lumana a Najeriya da kuma kira da a tattauna. Wakilan Texas Al Green da Joaquin Castro sun gabatar da wani ƙuduri da ke goyon bayan masu zanga-zangar ga Yan Majalisar Wakilan Amurka.